# The Health and Social Implications of Child Marriage in Nothern Nigeria
# Shigar Giza-Gizan da Addinin Musulunci da Al'adun Hausawa Suka Yi wa junannsu

Daga
**Abdullahi Aliyu Mai'adua**
Department of Nigerian Languages
Dr. Yusufu Bala Usman College, Daura

Da
**Sama'ila Muhammad**
Department of Nigerian Languages
Dr. Yusufu Bala Usman College, Daura

**Tsakure**

*Kowace al'umma ta duniya, sun yi imani da irin abubuawan bautarsu, kama daga addinin gargajiya har ya zuwa lokacin da addinin musulunci ya shigo qasar Hausa, haka kuma, akwai bambanci ta fuskar abin bautar da siga da kuma yanayin yadda ake yin bautar, kai har ma da lokaci yin bauta yana bambanta daga wani yanki na al'umma zuwa wani. A wannan takarda, an yi bayanin ma'anar addinin da Addinin musulunci da kuma ma'anar al'ada da kuma yadda addinin musulunci da al'adun Hausawa suka yi kamanci da kuma irin varnar da kowanensu ya yi ma wani. Sannan kuma, an kawo ra'in da aka xora binciken a kai, daga qarshe an kawo kammalawa tare da manazarta.*

---

Mabudai
Addini
Musulunci
Al'ada
Hausawa

## 1.0 Gabatarwa

Bautar ta farko da al'ummar Hausawa suka fara yi ita ce bautar addinin gargajiya, imanin Bahaushe shi ne yarda da akwai wata halitta boyayya, buwayayya mai ban tsoro wadda ta gagari saninsa (Bunza, 2006).

Haka kuma, kafin bayyanar addinin musulunci a qasar Hausa, babu wani abin bauta da al'ummar wannan lokaci suka sa a gaba illa ―bori‖, ―tsafi‖ da camfe-camfe da bukukuwa da buxar dawa da shan kabewa da hawan sadaka duk a matsayin su ne hanyar bautarsu (Bunza, 2006).

Kazalika, da addinin musulunci ya shigo qasar Hausa a wajen qarni na goma sha huxu (Q14), ya yi hani da horo a kan duk wata bauta wadda ba addinin musulunci ba ce (Galadanci 1992).

An bayyana cewa Larabawa da suka fara shigowa qasar Hausa, a wancan lokacin sun fito daga Arewacin Afrika ne kuma su ne suka kawo addinin musulunci qasar Hausa. Katsina ita ce qasa ta farko da Larabawa suka fara shiga cikinta, daga nan sai Kano. Wannan ya faru ne saboda hanyar da ta biyo Tumbuktu daga Arewacin Afrika (Sallau, 2009).

## 1.1 Ra'in Bincike

Ra'i wani bayani ne na ilimi wanda ke nuna tsarin yadda za a xora wani bincike a kai. Wasu masana na kallon ra'i a matsayin wani tunani ko hasashe ko bayani na ilimi wanda masana da manazarta ke yin amfani da shi a matsayin mizani na yin nazarce-nazarce a fadin duniya (Ado, 2017).

Wannan bincike an xora shi a bisa ra'in sassarquwar al'adu (cross – cultural Theory). Ra'i ne wanda wasu masana a qarni na 18, masu rajin ―Hauhawar Balaga/Hauhawar sauyi ko canjin hallitu‖ (Evolutionary Theory) suka bunqasa shi. Misalan su sun haxa da: Edward Burnett Taylor da Lewis Henry Morgan da George Peter Murdock. Ra'i ne da ake yin amfani da shi domin yin kwatance a tsakanin al'ummomi biyu ta hanyar kamance da gyare-gyare da shigar giza-gizai da suka yi wa juna. Wannan ra'i yana bayanin cewa al'adun al'ummomin duniya sukan cancanza a sanadiyar sarquwa da wasu al'adu ta hanyar cuxanya da juna. Hakan kan auku

ta sanadiyar qaura da mutane ke yi bisa wasu dalilai masu yawa, irin su neman ilimi, yaxa addini ko kasuwanci (Ado, 2017).

Bugu da qari, masana irin su Gusau (2015) da Garba (1984) da Yakubu (2017), sun yi amfani da wannan ra'i na (cross – cultural Theory) wajen gudanar da bincikensu.

To, a wannan bincike, an yi amfani da wannan ra'in wajen nazarin a kan addinin musulunci da al'adun Hausawa dangane da kamanci da kuma irin shigar gizai-gizai da kuma irin gyaran da aka samu sakamakon zuwan addinin musulunci a qasar Hausa.

## 2.0 Ma'anar Addini

Addini wata hanyar bauta ce da ke tafiya da imanin mutum na kusanta da Ubangijinsa, ko aljaninsa ko dodonsa da magabatansa. A wasu lokuta akan haxa da kaxe-kaxe, da aje-ajen wasu abubuwa kamar baqar akuya, jan zakara, farin kare (Gobir, 2017).

Addini shi ne hanyar rayuwa bisa bautar wani abin bautawa, bisa amfani da wasu tsare-tsaren da wannan abin bautar, ko kuma makusantansa suka tanadar, domin tafiyar da rayuwar yau da kullum ta mabiya wannan addinin, bisa wasu tanaje-tanaje ko tsare-tsare.
Haka kuma, akwai dalilan da ke sa ake yin addini, akwai neman sakamako da neman kariya daga miyagun al'jannu da abokan hamayya da kuma dokoki da tarbiya da kuma hukumce-hukumcen shari'a da bayyanar da gaskiya da riqon aman.

Kazalika, addini ya samar da kasha-kashe na addinin iri daban-daban irin su:

Addinin Gargajiya.

Maguzanci.

Arnanci.

Siddabaru.

Dabbanci.

Tsafi, bori da camfe-camfe (Gobir, 2017)

Bayan waxannan an samu addinai daban-daban sakamakon zuwan baqi a qasar Hausa, waxanda suka haxa da:

Addinin Musulunci, addinin Kiristanci da addinin Yuhudanci da Sauransu (Bunza, 2006).

## 2.1 Addinin Musulunci

Addinin musulunci addini ne wanda ya bayyana ta hanyar manzon tsira shugaban dukkan Musulmai, Annabi Muhammadu (S.A.W) ta hanyar mala'ika Jibirilu a kogon hira (Iqra'a) wato karanta (hira da malam Lawal Liman, 2018).

Kazalika, an ci gaba da saukar da ayoyi har aka haxa alqur'ani mai tsarki, wanda daga nan ne aka samu manyan mashahuran malamai Larabawa da sauran malamai daga qasashen Musulunci da dama sun shigo qasashen Afrika ta yamma da ta Arewa sun ziyarci qasashen Hausa domin yaxa addinin musulunci. Daga ciki akwai qasar Katsina, Kano da Zazzau. Addinin musulunci ya ci gaba da havvaka har inda ake a yau.

## 3.0 Mana'ar Al'ada

Al'ada tana nufin dukkanin rayuwar xan Adam tun daga haihuwarsa har zuwa kabarinsa (Bunza, 2006).

Al'ada hanya ce da ta qunshi dukkanin rayuwar mutum, wato abubuwan da mutum yake aikatawa na sarari ko na voye, da gavvansa ko a cikin zuciyarsa, ko a cikin harkokin rayuwarsa, tun daga haihuwarsa har zuwa mutuwarsa, to yana yin su a cikin ala'adarsa ne (Ado, 2017).

## 4.0 Gyaran da Addinin Musulunci Yayi a kan Al'adun Hausawa

Da addinin musulunci ya shigo qasar Hausa babu abin da ya tarar ana gudanarwa sai addinin bori da tsafi da camfi da bautar iskokai da wasu abubuwan bauta domin samun mafita a rayuwa.

Amma da addinin musulunci ya zo, sai ya yi hani da horo a kan duk wata bauta wadda ba addinin musulunci ya zo da ita ba. Misali; addinin musulunci ya yi hani da horo a kan gudanar da bori da tsafe-tsafe, tare da nuna cewa, addinin musulunci shi ne addinin Allah wanda zai kai al'umma ga mafita (hira da malam Lawal Liman, 2018)

**4.1 Gyaran da Addinin Musulunci Yayi ta Fuskar Bukukuwan Gargajiya** na Hausawa Lokacin da addinin musulunci ya shigo qasar Hausa babu bukukuwa da ake gudanarwa sai bikin buxar dawa, shan kabewa, hawan sadaka, da kalannkuwa, wa amma sai addinin musulunci ya yi gyara a kai, ya kawo bukukuwa irin su bikin sallah, saukar karatun alqur'ani, maulidi da bikin naxin shugaba, kamar irin su sarakuna, malamai da limamai duk addinin musulunci ya zo da su kuma ya yi hani da horo a kan bukukuwan gargajiya zalla.

Amma har yanzu akwai masu gudanar da bukukuwan gargajiya, a qasar Hausa kuma tsafi da bori, kuma su yi bautar addinin musulunci (hira da malam Alhassan, 2018).

### 4.2 Gyaran da Addinin Musulunci Yayi ta Fuskar Al'adun Mutuwa

Kafin zuwan addinin musulunci a qasar Hausa, al'umma ba su da ilimin da za su yi wa gawa sutura a rufe ta, sai dai su yi ta ajiyar ta. Misali, maguzawan Batsari da kaina – fara arnan Birchi sukan tsafa gawa su riqa yawo da ita duk inda za su, amma da addinin musulunci ya zo sai ya yi hani a kan wannan, kuma ya bayyana cewa idan za a rufe gawa sai an yi mata sutura, sannan a yi mata sallah da kaita kabari tare da yin wasu addu'o'i kamar yadda addinin musulunci ya zo da su (hira da Ibrahim Birchi, 2018).

### 4.3 Gyaran da Addinin Musulunci Yayi ta Fuskar Rabon Gado

Kafin zuwan addinin musulunci qasar Hausa, Hausawa ba su da ilimin addini wajen rabon gado. A lokacin idan mai gida ya mutu ya bar 'ya'ya maza da mata, mazan ne kawai ke da gado, har matan suma suna cikin dukiyar gado, wato ana raba su a matsayin gado.

Amma addinin muslunci ya zo qasar Hausa sai yay i gyara a kai, inda ya kawo tsarin yadda za a yi rabon gado. Misali: namiji ya kan samu kashi biyu bisa uku (2/3), mace kuma ta kan samu xaya bisa uku (1/3) (hira da M. Lawal Liman, 2018).

### 4.4 Gyaran da Addinin Musulunci Yayi ta Fuskar Raxin Suna

Kafin zuwan addinin musulunci Hausawa suna zanen suna ko raxin sunayen ya'yansu kara zube, duk sunan da aka samu sai a raxa ma jariri ko jarirya. Amma da addinin musulunci ya zo,

sai ya zo da bayanin yadda za a raxa suna. Misali; sunayen sahabbai, Umar, Abubakar da kuma sunayen

Annabawa irin su Isma'il, Musa, Isa. Ba kamar yadda ake raxa suna ba, a al'adu irin su mai Damma, Ci wake, Ranau, Audi, Cindo, Dare, Sammako. Duk zuwan addinin musulunci ya kawar da waxannan sunayen (Alhassan, 2018).

## 5.0 Kamanci Tsakanin Addinin Musulunci da Al'adun Hausawa

Idan muka kalli tsarin yadda Hausawa ke gudanar da al'adu ta fuskar zamantakewa akwai kamance tsakanin addinin musulunci da al'adun Hausawa, misali:

camfi yana da kamanci da addinin musulunci, saboda kamar yadda camfi ke nuna hani ko horo a kan kar a aikata wani abu mummana, ko marar kyau wanda idan ma an aikata abin wani abu na iya samun wanda ya aikata abin. To haka ma addinin musulunci yake da dokoki wanda idan an karya su ana iya samun sakamako marar kyau a ranar gobe qiyama (hira da Alhassan, 2018).

Haka kuma, akwai hanyoyin tarbiya da ladabi da biyayya da kunya da gaskiya da riqon amana da kara da tsare mutunci da bin nag aba, wanda duk akwai su a tsarin al'adun Hausawa da zamantakewarsu kuma addinin musulunci, ya aminta da su, kuma ya bada damar a ci gaba da aiwatar da su saboda da kyawawan xabi'u ne (hira da M. Lawal Liman, 2018).

Haka kuma akwai kamance a tsakanin addinin musulunci da al'adun Hausawa ta fuskar karin magana da Hausawa ke gudanarwa. Misali:

―Hassada ga mai rabo, taki‖.

―Binn na gaba, bin Allah‖.

―Duk zakaran da Allah ya nufa da cara, ko ana muzuru ana shaho, sai ya yi".

Saboda haka da addinin musulunci ya zo qasar Hausa ya tarar ana amfani da karin magana iri dabandaban. Idan aka lura addinin musulunci ya yi magana game da munin hassada a wurare da dama a cikin Alqur'ani da Hadisai. Sannan kuma ya nuna duk abinda Allah ya tsara sai ya faru a rayuwa (hira da M. Lawal Liman, 2018).

## 6.0 Addinin Musulunci da Al'adun Hausawa da Varnar da Suka yi wa Kowanensu

Idan muka dubi zuwan addinin musulunci qasar Hausa, babu abin da ya tarar ana gudanarwa sai addinin bori da tsafe-tsafe da camfe-camfe da girka da bautar iskokai da bautar kan gida da biyayya ga sarakunan tsafi da bukukuwan da ba na addinin musulunci ba daga maqiya da miyagun aljannu da abokan gaba.

Amma da addini musulunci ya zo sai ya nuna cewa gudanar da waxanan abubuwann haramun ne, babu su a tsarin addinin musulunci. Kuma ya kawo irin abubuwan da ya kamata a yi su, a matsayin bauta, irin su: Sallah, Hajji, Zakka, Imani, Azumi da sauran abubuwan da addinin musulunci ya yarda da su (Hira M. Lawal Liman,2018).

Haka kuma, idan muka lura da al'adun Hausawa za mu ga cewa wasu al'adun sun mamaye zukatun mutane, wanda har yanzu ana gudanar da su. Misali; zaka ga mutum musulmine, ya yi sallah kuma ya yi bautar iskoki da bori, da tsafe-tsafe. Wannan varna ce ga addinin musulunci. Ta hanyar bukukuwa ma, har yanzu akawai bukukuwan maguzanci da wasu mutane ke aiwatarwa kuma suna sallah. Misali: Bikin Hawan Sadaka, buxar dawa, shan kabewa. Ajon bori da sauransu.

Haka kuma, addinin musulunci da ya zo ya yi hani da horo a kan duk wata bauta, in ba Allah (S.W.T), wanda babu wani abin bauta da gaskiya sai shi (Hira da Alhassan, 2018).

Haka kuma, a wannan zamani da muke ciki, za mu ga cewa wasu manyan malamai masana Alqur'ani da Hadisai da ilimin Fiqhu duk sun yi wa addinin musulunci varna, sun fake da al'adun bokanci da tsubu da aiki da rufanai da aljannu da dodo da rufa-ido domin samun abin duniya, wai kuma musulmi ne suna sallah. Wannan varna ce da wasu malamai suka yi wa addinin musulunci (Hira Malam Lawal Liman, 2018).

Ta fuskar girkar bori za a ga cewa addinin musulunci ya fatattaki al'adun girka na sannya iskokai ga mutane da niyyar neman waraka daga wata cuta. Sai ya zo da ruqiya ta hanyar amfani da ayoyin Alqur'animai girma domin fitar da iskoki.

**7.0 Kammalawa**

Haqiqa. Addinin musulunci ya yi namijin qoqari wajen kawar da al'adun Hausawa da xabi'unnsu marassa kyau, irin su addinin bori, tsafe-tsafe da bukukuwan da ban a musulunci ba. Amma a yanzu sai 'yan gutsiri tsoma‖, wato 'yan tava kixa tava karatu‖ wavanda suna sallah amma suna bautar iskokai da bori saboda abin ya mamaye zukatunsu.

A cikin wannan bincike an kawo gabatarwa da kuma irin ra'in da aka xora binciken a kai. Sannan kuma kawo ra'ayoyin masana akan ma'anar addinin, ma'anar addinin musulunci da kuma ma'anar ala'da.

Kazalika, an kawo irin gyare-gyaren da addinin musulunci yayi a kan al'adun Hausawa da kuma inda suka yi kamanci da kuma yi wa abin kwaskwarima. Daga qarshe an kawo wuraren da kowanensu yayi wa kowane varna, sannan aka kawo kammalawa tare da manazarta.

**Manazarta**

Ado A. (2017) Ra'o'in Bincike kan Al'adun Hausawa. Katsina: Kankiya Classical Media Enterprises.

Bunza, A. M (2006) Gadon Fexe Al'ada' Lagos: Tiwal Nigerian Limited.

Galadanci Da Wasu (1882) Hausa don Qananan Makarantun Sakandire, Nigeria, Longman, Nigerian Plc.

Gobir, A. Y (2017) Laccar Kwas ―NLH 8322. Approach to the Study of the Religion and culture. (Dangantakar Addini da Al'ada). A Ajin Masu Neman Digiri na Biyu (MA) Katsina: Jami'ar Umaru Musa Yar'adua.

Gusau, S. M (2015) Mazhabobin Ra'i da Tarke a Adabi da Al'adun Hausawa Kano Centaury Research and Publishing Limited.

Sallau, B. A (2009) ―Sana'ar Wanzanci Da Sauye-Sauyen Zamani Jiya da Yau ―Kundin Digiri na

Ukk (Ph.D), Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya Jami'ar Bay